# DEUTSCHE WELLE
# JI KA KARU

## Almara a Afirka domin al'adu da zaman lafiya:
## Bari na ba ku labari
## Na shida: Sarki babu masarauta


| | |
|---|---|
| Wanda ya rubuta: | Ibrahima Ndiaye |
| Waɗanda suka tace: | Yann Durand, Stefanie Duckstein, Naïma Guira |
| Wanda ya fassara: | Ɗanlami Bala Gwammaja |


**'Yan wasa:**

Mai ba da labari

Ahmad

Tsohuwa

Mamman

MAI GABATARWA:

Masu sauraronmu, barkanmu da sake saduwa da ku a cikin kashi na shida a cikin shirinmu na “Ji Ka Karu” mai taken “Bari Na Ba Ku Labari”. Shi wannan shiri ne a kan hikayoyin Afirka masu koya zamantakewa tsakanin al’umma. Hikayoyi dai labaru ne na gargajiya waɗanda suke burge yara da manya. Kuma sukan nuna yadda ɗan Adam kan tafiyar da rayuwarsa.
A shirin namu na yau za mu ji yadda wani yaro ɗan baiwa ya dawo gida. Sai ku karkaɗe kunnunwanku ku sha labarin “Sarki babu masarauta”.

MAI BA DA LABARI:

A shekaru masu yawa da suka wuce, an yi wani sarki adali da ya yi mulki a wata ƙasa da ake kira Ginuwa. Ita dai Ginuwa ƙaramar ƙasa ce, amma fa tana da ƙasar noma mai kyau, kuma kowa yana jin daɗi a ƙasar. Ana nan sai wata rana matar sarki, wato sarauniya, ta haifi kyakkyawan ɗa namiji mai kuzari, wanda aka sa wa suna Ahmad. Sai dai kuma ba a daɗe ba sai murna ta koma ciki. Domin kuwa wata rana sarki ya fita farauta, sai wata ƙatuwar mage ta far masa, har ta ji masa mummunar rauni, wanda ya yi sanadiyyar ajalinsa. Ba a kai ma ga binne shi ba, sai aka fara raɗe-raɗin wanda zai gaje shi. Ahmad dai shi ne ya kamata a ce ya hau wannan karaga, sai dai kuma bai riga ya kawo ƙarfi ba. Nan da nan sai wani mai mulkin kama-ƙarya ya hamɓarad da shi, kuma ya tilasta masa gudun hijira nesa da daular Ginuwa.

Ahmad dai bai ji daɗin wannan abu da ya faru ba, to amma tun da bai kai ƙarfin da zai yaƙi abin ba, sai ya rungumi ƙaddara. Ana nan ana nan, shekara da shekaru, har Ahmad ya tashi ya zama kyakkyawan saurayi, wanda kowa yake yabawa da shi. Daga nan sai ya auri wata yarinyar kirki mai suna Fatima, wadda ta haifa masa kyawawan ’ya’ya.

Waɗannan ma’arauta suna nan suna ci gaba da zamansu cikin kwanciyar hankali, kwatsam sai wata shekara aka yi fari a ƙasar. Bayan an shafe watannin ana wannan fari, har sai da ta kai babu sauran abinci a ƙasar. Sai Ahmad ya ji tsoron kada iyalinsa su

hallaka, don haka dolensa ya fice ya nufi wata ƙasar da bai sani ba. Shi dai abin da yake fata shi ne, Allah ya sa ya samu isasshen abincin da zai ciyar da iyalinsa. Ya san dai da an taɓa cin amanarsa, anya kuwa shi ma yanzu ba cin amanar 'ya'yansa yake yi ba? Su ma fa sun cancanci su rayu cikin mutunci. Kafin ya tashi ya bar ƙasar, sai da matarsa Fatima ta ɗaukar masa alƙawarin kula da yaransa idan ya tafi.

Gari na wayewa da asuba, sai Ahmad ya kama hanya. Ya yi tafiya mai nisa, ya tsallake koguna da ƙasashe masu yawa waɗanda bai ma taɓa saninsu ba. Duk da wannan wahala, Ahmad ya kasa tara wani abin kirkin da zai koma gida ya kai wa iyalinsa. Inda abin ya daɗa munana ma shi ne, ga shi ba abin da ya dame shi irin gajiya da kuma yadda zai kaucewa kamuwa da cututtuka.

Wata rana sai ya buƙaci ya ɗan huta, sai ya samu wata babbar bishiyar kuka ya zauna a gindinta. Bayan ya ɗauko goransa ya kurɓi ruwa, sai ya fara tunanin abin da ya fi dacewa da shi a rayuwarsa. Shi dai Ahmad bai san ma me zai yi ba yanzu. Wato ke nan yanzu duk abin da ya yi tunani a rayuwarsa ya watse ke nan? Da yake ya riga ya gaji liƙis, sai kawai barci ya kwashe shi.

A lokacin da ya farka, rana tana shirin faɗuwa. Da ya sake kama hanya, sai ya hango wata tsohuwa a nesa tana tafiya da ƙyar. Da alamun wannan tsohuwar ta gaji liƙis, ga kuma tsananin ƙishi a tare da ita. Nan da nan sai Ahmad ya tafi don ya taimaka mata.

AHMAD:

"Allah sarki, Baba, me ya faru? Zo nan, bari na taimake ki. Mu je gindin waccan bishiyar. Ya kamata ki huta don ki mai da numfashinki."

MAI BA DA LABARI:

Sai Ahmad ya kai wannan tsohuwar gindin bishiya ya zaunar da ita, ya ba ta ruwa ta sha, har ma kuma ya ba ta duk abincin da ya mallaka. Bayan da tsohuwa ta samu kanta, sai ta ce da Ahmad:

TSOHUWA:

“Wallahi na gode! Wallahi ɗan samari, ka ceci rayuwata. Wasu ne suka yi min fashi a hanya, suka ƙwace ’yan kayana. Kai kuwa me kake yi a nan kai kaɗai?”

AHMAD:

“Gaskiya labarin yana da tsawo. Kin riga kin dai san yadda rayuwa take da wahala. Ni dai na baro iyalina tun da daɗewa don neman arziki. Amma kin ga yanzu ma na daɗa talaucewa fiye da da!”

TSOHUWA:

“Tun da dai ka taimake ni, yanzu ni ma zan taimaka maka. Zan ba ka wata shawara, kuma kar ka kuskura ka manta da abin da zan gaya maka. Shawarar kuwa ita ce: Kada ka kuskura ka yi abin da ya fi ƙarfinka. Idan ka bi wannan shawara tawa, za ka cim ma burinka.”

MAI BA DA LABARI:

Daga nan sai wannan tsohuwa ta tafi ta bar Ahmad, ya yi mamaki, kuma ransa ya sosu. Shi a tunaninsa ma wataƙila wannan tsohuwa mahaukaciya ce. To bayan wani ɗan lokaci, sai ya hango wata guguwa daga nesa.

Can kuma sai ya hango dawakai da yawa suna biye da wani a kan ingarman doki shi kaɗai sanye da kaya irin na sarauta. Sauran dawakan da ke biye da shi na ɗauke da jakunkuna cike da gwala-gwalai. Shi wannan mahayi ya tsaya kusa da Ahmad ya ce masa:

MAMMAN:

“Abokina, sannu da hutawa!”

AHMAD:

“Sannu kadai, yallaɓai!”

MAMMAN:

"Sunana Mamman. Ni ne ɗan autan Sarkin Ginuwa, wanda bai daɗe da mutuwa ba. Amma kuma ban yi wani baƙin ciki ba saboda azzalumi ne. Yanzu yayana ne ya gaje shi, kuma shi ma azzalumi ne kamarsa. Sai dai kuma na gaji arziƙin nan da kake gani, kuma na yanke shawarar kwashe kayana na doshi wata nahiyar."

MAI BA DA LABARI:

Ahmad ya yi mamaki da jin wannan magana, da kuma abin da ya gani, ta yadda har ma ya kasa tuno da masarautar da Mamman ya ambata.

MAMMAN:

"Kana ji ko abokina, zan yi maka wani tayi, don kuwa na lura cewa saboda wannan arziƙin da kuma gwala-gwalan da nake ɗauke da su, yanzu na zama abokin ɓarayi da 'yan fashi.
Don haka ina so ka raka ni mu yi wannan tafiya don ka dinga kare lafiyata. Ni kuma zan ba ka rabin dukiyata. Don ni har yanzu ban ga wanda na amince wa ba, amma na lura kamar kai mai gaskiya ne. Saboda haka da zarar ka yi min mubaya'a, to rabin dukiyata ta zama naka."

MAI BA DA LABARI:

Nan da nan sai Ahmad ya fara tsuma saboda ɗoki. Anya kuwa ba wannan ce sa'ar da ya fito nema ba kuwa?

AHMAD

"Gaskiya na yi murna da wannan tayi da ka yi min. Lalle ni mutum ne mai gaskiya, kuma na yi maka alƙawari zan tafi tare da kai. Kuma na yi alƙawari zan yi maka biyayya."

MAMMAN:

"To yi maza ka hau doki, na ji daɗin gamuwa da kai. Zo ka hau

wannan goɗiyar. Kuma daga yau ta zama mallakinka."

MAI BA DA LABARI:

Sai Ahmad ya ɗare goɗiya, kuma ya ji kamar an naɗa masa sarauta. Yana hawa sai ya fara lura cewa, ashe fa a cikin wani kyakkyawan wuri yake, bai ma lura ba. Wannan sa'a da ya samu ji yake abin kamar a mafarki.

AHMAD:

"Yanzu dai kam ni na samu sabon aboki, kuma nan ba da daɗewa ba zan koma wajen iyalina a matsayin mai arziƙi."

MAI BA DA LABARI:

A tsawon lokacin da suka yi suna tafiya, sun sha gwagwarmaya dabam-dabam, kuma Ahmad ya nuna cewa shi jarumi ne kuma abin dogaro. Wata rana sai suka zo wani ƙaton kogi wanda ya ɗauke su lokaci mai tsawo kafin su samu wurin da ba shi da zurfi su haye.

MAMMAN:

"Ahmad, shiga ruwan nan ka ga yanda zurfinsa yake. Ba na son gwala-gwalanmu su bi ruwa."

AHMAD

"To, abokina. Ga ni nan zuwa."

MAI BA DA LABARI:

Sai dai kuma Ahmad bai iya ruwa ba, amma yana so ya nuna biyayyarsa ga Mamman. Yana shirin zai faɗa cikin ruwan, sai ya tuno da maganar tsohuwar nan cewa: "Kada ka kuskura ka yi abin da ya fi ƙarfinka!" Sai ya dakata na wani ɗan lokaci. Daga nan sai ya nuna wa Mamman cewa shi fa bai iya ruwa ba.

MAMMAN:

"Hahaha! Ni da nake neman wanda zai kare lafiyata, ashe matsoraci na samo! Ni me ya sa ba ni da sa'a ne a rayuwata? Ga ni da gwala-gwalai ba iyaka, amma duk da haka sai da kaina zan yi kome?"

MAI BA DA LABARI:

Don haka sai Mamman ya kwaɓe ya faɗa ruwa. Har sai da ya kai yana taɓo ƙasan ruwan. Bayan da Mamman ya haye ruwan, sai ya juyo yana ce wa Ahmad ya biyo ta inda ya tsallako tare da dabbobinsu. Kwatsam sai wani kada ya biyo ta bayansa ya kashe shi.

Nan dai Ahmad ya mace a tsaye, domin kuwa ba abin da zai iya yi. Bayan da ya samu kansa daga wannan kiɗimewa da ya yi ta rashin abokinsa, sai ya fara tunanin, yaya zai yi. Don kuwa yanzu dai ga shi yana da arziki mai yawa a hannunsa. To amma shin mene ne abin da ya fi dacewa ya yi? Can sai ya tuna abin da zai yi. Ashe fa Mamman ya taɓa ambatar sunan daular Ginuwa. Don haka sai ya gane cewa ashe fa shi Mamman ɗa ne ga wanda ya ƙwace wannan daula a hannunsa! Nan da nan sai ya fahimci cewa ya kamata fa a mayar da dukiyar nan ta Mamman ga talakawan ƙasar, waɗanda azzalumin sarkin nan, wato uban Mamman, ya zalunta. Sai ya tattara dukkan dabbobin nan ya kama hanyar gida.

Bayan ya daɗe yana tafiya, sai ya tsaya a Maƙera, wadda wata daula ce da ya sani tun yana ƙarami. Sarkin da ke mulkin wannan daula, wato Sultan, ya yi masa kyakkyawar tarba, domin da ma can abokin babansa ne. Ahmad ya bayyana wa Sultan duk abin da ya faru, da kuma abin da yake nufin yi.

AHMAD:

"So nake na je Ginuwa, wato garin babana, na mayar wa da talakawa abin da aka ƙwace musu."

MAI BA DA LABARI:

Nan da nan sai Sultan ya ji yana ƙaunar Ahmad, domin kuwa maganar Ahmad ɗin ta shige shi. Don haka sai ya karrama shi a

fadarsa, kuma ya sa aka yi gadin dukiyar nan da yake ɗauke da ita, sannan kuma aka kula da dawakansa. Bayan wasu makonni, lokacin Ahmad ya murmure daga gajiyar tafiyar da ya sha, sai Sultan ya ba shi wasu dakaru don su taimaka masa, tare kuma da garken shanu don ya samu damar ƙwato sarautar daular Ginuwa.
Daga nan sai Ahmad ya kama hanya tare da dakarunsa da kuma dabbobinsa, suka nufi babban birnin Ginuwa. Nan da nan sai labarin dawowar Ahmad ya cika gari, har ya kai ga kunnen yayan Mamman. Ya ji ana kwatanta Ahmad da mutum ne kyakkyawa mara tsoro, wanda ke da niyyar raba dukiyarsa ga talakawan Ginuwa. Sai tsoro ya kama shi har ma ya tsere daga fadar. Shi kuwa Ahmad sai mutanen Giniwa suka yi masa kyakkyawar tarba. Kuma ba a daɗe ba suka mayar da shi ya zama sabon sarkin Ginuwa. Daga nan sai ya yi musu jawabi yana mai cewa:

AHMAD:

"To da farko dai ina so na mayar muku da dukiyarku da aka ƙwace muku. Ga ta nan, ku yi amfani da ita don ci gaban kowa da kowa!"

MAI BA DA LABARI:

Ahmad na tsaye a gaban taro, sai ya yi magana da babban bafadensa:

AHMAD:

"Ina so ka aika a zo mini da iyalina nan. Ba zan sake yarda na rabu da su ba. Kuma a taho min da aminina Sarki Sultan na Maƙera, wanda da ma aminin babana ne. Ina gayyatar kowa ya zo don a yi wannan shagali!"

MAI BA DA LABARI:

Bayan wasu shekaru masu yawa, sai Ginuwa ta sake dawowa matsayinta na ƙasa mai zaman lafiya da ni'ima. Ahmad dai kam bai sake yarda sun rabu da iyalinsa ba.

MAI GABATARWA:

Da haka ne kuma muka kawo ƙarshen hikayarmu mai suna "Sarki babu masarauta" wanda labarin wani mutum ne da ya taɓa rasa kome kuma daga baya arziƙinsa ya dawo, saboda taimaka wa mutane da ya yi, kuma ya karɓi shawararsu. Shin ko kun taɓa fuskantar wani yanayi da jin shawara ya yi muku rana? Sai ku aiko mana ta adireshinmu na yanar gizo, wato www.dw-world.de/lbe. Ibrahim Ndiaye ya rubuta wannan hikaya.